# Zogalagandi, tambaya mai yawa, samuwar ta kalilan

Zogalagandi ko zogala ko zogale ko kuma tamaka ko yal (yar) makka yanda ake kiran ta a kasar hausa, wadda Zabarmawa ke ce ma windi bundu. A cikin wannan watan na satumba, za a ga manyan motoci shake da buhunnan zoga la inda mata yan kasuwa ke rububinta a kasuwannin birnin Niamey. Muna cikin lokacin damana, wato daidai lokacin noman ita wannan zogala. Su dai mazamna birnin Niamey sun shahara wajen cin wannan ganye na zogala mai kumshe da bitamin, da karhe, da sinadirori da sauran furotoyin. In an duba ko suna da gaskiya, domin garam 100 na danyen ganyen zogala na samar da furotoyin kin da kwai daya ke badawa, haka daidai da sinadirorin kalsiyom da za a samu a finjalin madara guda. Ko kuma daidai da yawan karhen da za a samu a tsagin nama. Idan ko aka duba garam 100 na ganyen zogala ba shi da yawa. A karshen watan takwas (août) na 2010 ana saida kashin zogala a kan kudi cfa 400 a karamar kasuwar Niamey, wanda kashin ya yi daidai da rauyin 2,5 kg a misali. Wannan ko za ya yi daidai da kwayaye da finjalan madara masu dinbin yawa.

## Gyaran ta da kyau

Kamar sauran ire-iren cimaka, matsalar daya ce ta wajen dahuwar ta inda take son kulawa don kar a rasa sinadirorin da ta kumsa na gina jiki, kamar su bitamin da ke lalacewa lokacin dahuwarta. Ana ba da shawarar a yi saurin cin ganyen zogala bayan an tsigo shi, sannan wajen dahuwar kar ta dau lokaci mai tsawo. Yana kuma da kyau a adana ruwan nan da aka dafa ta (ruwa ko miya) wato bayan an dafa. Bayanan da aka samu na game da ruwan da aka dafa ta, suna da dadin sha ne. Yin kuma garin ta, wata hanya ce mai kyau con adana abubuwan da ta kumsa na gina jiki (ko da yake ana asarar su lokacin da aka shanya ta), ana iya yin anfani da wannan gari bayan an dafa abinci. Garin zogala na kumshe da furotoyin, bitamin, da sauran sinadirai, wadanda ya kamata a yi anfani da su.





**Kasar Nijar, kasar zogala, na fama da karamcin ta**

Wannan ko haka ne, abun da ban mamaki. Wai kasar Nijar na kawo zogala mai yawa daga makwabciyarta Nijeriya. Babbar Kungiyar nan ta kasar Amuruka mai kula da kananan kungiyoyin da ke kula da kyautata tsarin noman zogala a Nijar (CLUSA), ita ce ta kiyasta yawan busassar zogala da aka shigo da ita daga Nijeriya ya kai tan dubu goma (10.000). Abin ya kazamce, don babban arziki ne da ya kubce ma manoman Nijar.

Kasar Nijeriya na noman zogala musamman a lokacin damana. Su ko yan kasuwar Maradi sai su je a wannan lokacin su saro zogala busassa inda za su saida ta daga baya a cikin kasuwannin Niamey. Bayan haka, daga nan Maradin dai, ana aika zogalar a kasashen Moroko, da Aljeriya, da Saudiya, har ma ya zuwa kasar Cana (Chine).

Akwai da yawa daga cikin manyan yan kasuwa da suka kware wajen kasuwancin ta, inda wasu daga cikin su suke da karfin ajiyar fiye da buhu dubu biyar (5.000) a lokaci guda. Babban buhu na ganyen zogala da aka sulala, aka shanya, ana saida shi a kasuwar Maradi, cikin watan takwas (Août) a kan kudi cfa 20.000. A kasuwar Niamey ko, ana saida irin wannan buhun amma na danyar zogala da aka noma a cikin lambuna, a kan kudi cfa 5.000.

**Ya cancanta a kara yawan noman ta a kasar Nijar**

Kungiya ce mai zaman kanta, wato Babbar Kungiyar nan ta kasar Amuruka mai kula da kananan kungiyoyin da ke kula da kyautata tsarin noman zogala a Nijar (CLUSA), ta fara wani Shiri da ke kula da noman zogala a Nijar. Shi dai wannan Tsari, wanda za ya dau tsawon shekara uku, babbar manufarsa ita ce " karfafa cimakar kasar Nijar ta hanyar kawo taimakon zogala don inganta cimakar, da kyautata abubuwan gina jiki ".

Shi dai wannan Shirin yana tafiyar da ayyukansa cikin jahohi guda shidda a nan Nijar : Niamey, Maradi, Tillaberi, Dosso, Tahoua da Zinder, inda yake kula da manoma wanda adadinsu ya kai dubu bakwai (7.000) a cikin shekarar 2010.

Ita dai kungiyar CLUSA na aiki da hadin gwiwar ma'aikatu hudu (4) a tafiyar da wannan Shiri : ICRISAT don horar da manoma a kan fusahar noma ; sai APOR wato ONG ce mai kula da habaka kungiyoyin karkara, don kawo taimako wajen tsara ayyukan manoman ; da kuma HKI don ba da tarbiyar abubuwan gina jiki ; daga karshe, sai Kokari don samar wa manoma bashi.

A farkon Shirin, CLUSA sai da ta sayi kilo 60 na iri wajen ICRISAT a kan kudi cfa 50.000 kowane kilo. Shi ne irin da aka ba manoman don su noma shi da yawa, inda su kuma za su rarraba wa mambobin rukuninsu kyauta. Haka kuma su dai wadannan manoman iri suna iya sayar da shi a duk mutumen da ke bukatar wannan iri, gwargwadon yawansa da ake da shi.

Tambayar na nan, samuwar ta ko kadan ce. Manyan wuraren noman ta su biyu ne, wato Maradi da kewayenta da kuma Niamey da kewayenta. Bayan tambayoyin da aka ma manoman zogala, sun kwatanta noman ta na da anfani, mai yawa kuma.

Duk da haka, kamar sauran abubuwan noma, zogala na bukatar kyautata wuraren noman ta.

Ma'aikatar nan ta kasa da kasa mai kula da bincike kan ayyukan noma a wurare masu zahi (ICRISAT), tana aiki bisa irin zogala kashi uku tun shekarar 2003 : iri guda shi ne ake kira PKM-1 (da ya fito daga Indiya), iri guda ya fito daga kasar Habasha (Ethiopia), sai iri na uku da ake kira zogalar sahara (peregrina), wanda ya fi dacewa da wurare kekasassu.

Bayan gwaje-gwaje da aka yi, an tambayi dukkan manoman ta da wadanda suke cin zogalar, sun yaba matuka da irin nan na PKM-1. Iri ne da ke badawa duk tsawon shekara. Kuma iri ne mai zahin toho inda za a iya tsigar ta duk kwana 15, ganyenta na da fadi, dandanonta ya fi na wannan ta gida dadi. An fara noman irin wannan zogala tun shekarar 2009 duk cikin jahohin Nijar, ban da jahar Diffa da jahar Agadas, da taimakon tsarin nan na Babbar Kungiyar Amuruka mai kula da zogala (CLUSA).

**Ita ma zogala an kyautata hanyarta ta fusaha**

Ya cancan a daidaita tsakanin shuka da shuka. ICRISAT na ba da shawarar a tsakaita bisa kan 2m x 2m don wadatuwar ganye. Tsari iri biyu na yiwuwa : sa iri kai tsaye daga kwaya 2 zuwa 3 a kowane rami ko kuma gyara hilin dashe da ke daukan tsawon kwana 35 zuwa kwana 45 kafin a dasa su cikin rami da ke da girman 30cm x 30cm.

Lokacin da dashen ya kai tsawon 60 cm, ko kuma bayan sati 2 ko 3, ya wajaba manomin ya yi muntsuna, wato ya cire tsiron shukar. Wannan dubarar na sa shuka ta yi sabbin rassa, inda aka ce rassa to an ce ganye mai yawa. Maimaikon a tsige ma reshe ganyansa, ya fi dacewa a datse rassa in sun kai tsawon 1m20 daga kasa (a dubi hoto na gefe). Dashen zogala da aka gyara na iya ba da isasshen



ganye da ya kai nauyin kilo 5 a kowace tsiga da za a yi.

Iccen zogala na iya rayuwa har tsawon shekara 15 yana ba da anfani, inda daga nan za ya soma ragewa, wato ganyensa za ya ragu. Amma don cin anfaninsa da kyau, ya kamata a rika sa masa taki kai a kai. Tukon kafin a dasa shi, ICRISAT na ba da shawarar a sa a kowane rami cikin hannu biyu na takin nan compost da kuma rairai cikin hannu hudu (4). A lokacin da ake aikin noman, a kowane gurbi a sa sheburori (pelo) 2 na compost tare da garam 100 na triple 15 a duk wata shidda.

**Shi ko matsayin mata ?**

Musamman mata ke sayar da zogala ga masu bukatar ta a kasuwannai. Ba a samun mata wajen bangaren kasuwancin zogala na yawan buhuna ko kuma bangaren ayyukan noman ta, tun da mata ba su da gonakin da za su rike suna noma su musamman irin wannan shuka ta zogala mai daukan tsawon shekara fiye da 15, ta kuma hade da wata shukar.

Yanzu dai, a cikin jahar Maradi, musamman ana gyara zogala mai yawa don adano. Aiki ne da mata ke kula da shi bayan sun sayo ta danya, sai su sulala ta kafin su shanya ta bushe. Ita ce za su saida wa yan kasuwa.

RECA-INFO
Bulletin d'information trimestriel du Réseau National des Chambres d'Agriculture du Niger
(RECA – Niger)
BP : 686 Niamey - Tél : 00227 21 76 72 94
Fax : 00227 20 72 38 68 - Email : recaniger@yahoo.fr
Site Internet :www.recaniger.org
Votre avis, vos suggestions, vos témoignages nous intéressent.
Écrivez-nous RECA BP 686 Niamey-Niger recaniger@yahoo.fr
Seuls les courriers nominatifs avec adresse et téléphone seront publiés
Directeur de la Publication
Bello Boubacar
Rédacteur en Chef
Youssouf Mohamed Elmoctar
Coordonnateur de la Rédaction
Amadou Boukari
Rédaction
Patrick Delmas
Aïssa Kimba
Dan Marafa Boubacar
Habou Mamane
Impression
Nouvelle Imprimerie du Niger (NIN)
Tél : 20 73 47 98
Ce numéro est tiré à 2000 exemplaires